

# Alherin Allah a fannin Kuɗi

*Yesu ya ɗauki talaucin mu domin mu sami yalwarsa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Akwai ƙa'idodi guda uku na musamman da ke zama jagora ga aikin alherin Allah. Na farko, ba za a taɓa yin aiki don samun alheri ba; akasin haka, duk abin da za a iya samu ta wajen aiki ba alheri ba ne:

> "In kuwa na alheri ne, ba sauran cewa ya dogara ga aikin lada ke nan [abin da muka yi wahalarsa]; in ba haka ba, ashe alheri ba alheri ba ne kuma.." (Romawa 11:6)

Wannan ƙa'ida ta ware yawancin mutane "masu addini" daga alherin Allah, domin suna ganin za su iya yin aikin samun sa.

Na biyu, akwai hanyar samun alheri guda ɗaya kawai. "Domin Shari'a ta hannun Musa aka ba da ita, amma alheri da gaskiya kuwa ta wurin Yesu Kristi suka kasance" (Yohanna 1:17). Duk wani nau'in alherin da ya zo mana ya zo ne ta wurin Yesu Kristi kawai.

Na uku, akwai hanya ɗaya tak da za mu iya samun alherin Allah, ita ce bangaskiya. An taƙaita wannan gaskiyar a cikin ayoyi uku a jere a cikin Afisawa 2:8–9: "Domin ta wurin alheri aka cece ku saboda bangaskiya,... ba ƙoƙarin kanku ba ne [abin da muka yi aiki muka samu]."

Krisa kaɗan ne suka fahimci cewa wannan ƙa'idar ta shafi fannin kuɗi da kayan more rayuwa ne kamar yadda take a kowane fanni na rayuwar mu. Littafi Mai Tsarki ya yi mana gargaɗi musamman game da:

- Rashin sanin ya kamata (Misalai 10:4);
- Ragonci (Misalai 24:30–34); da kuma,
- Rashin aminci (Afisawa 4:28).

Muddin muna da laifi a cikin waɗannan ɗabi'un zunubi, to, ba mu da damar sa zuciyar cewa alherin Allah zai yi aiki a ɓangaren rayuwar mu ta kuɗi. Saboda haka, a matsayin mu na Krista, dole ne mu kasance masu gaskiya, masu aiki tuƙuru, da kuma masu sanin ya kamata.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa a kan gicciye, Yesu ya ɗauki talauci na ya kuma

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

ba da alherin Allah a gare ni a fannin kuɗi da kayayyaki domin Yesu ya ɗauki talauci na domin in sami yalwarsa.

Amin.

**Abincin Yini ★**

Kwafi: WD-B097-130-HAU
Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026
Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc. 